Kabar abinda kake kokwantansa, zuwa ga abinda baka kokwantansa

Daga Abu Muhammad al-Hasan ibnu Ali Ibnu Abi Ɗalib - jikan Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - kuma abin shinshinarsa -, ya ce: Na haddace daga Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -: «Kabar abinda kake kokwantansa, zuwa ga abinda baka kokwantansa».

[Ingantacce ne] [Timizi da Nasa'i ne Suka ruwaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya yi umarni da barin abin da kake kokwanto akansa na maganganu da ayyuka cewa shin an hana kuwa ko a'a, shin haramun ne ko halal ne, zuwa ga abin da baka kokwanto a cikinsa daga abin da ka tabbatar da kyawunsa da kuma halaccinsa.

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/66519